# Dokar Bada Agajin Gaggawa ta Tarayya da Gudanarwar Harkokin Albarkatun Jama'an NYC na COVID-19 Takardar Shaidar Tsarin Tallafin Rasuwa

**Ta yaya zan nemi Tallafin Dokar Bada Agajin Gaggawa ta Tarayya (Federal Emergency Management Act, FEMA) ko Tsarin Tallafin Rasuwa na Gudanarwar Harkokin Albarkatun Jama'an NYC na COVID-19 (NYC Human Resource Administration, HRA) COVID-19 shirye-shiryen Taimakon Binnewa?**

- Don neman Tallafin Tsarin Bizinar FEMA na COVID-19, ziyarci fema.gov/disasters/coronavirus/economic/funeral-assistance.
- Don neman Tallafin Tsarin Bizinar NYC HRA na COVID-19, ziyarci www1.nyc.gov/site/hra/help/burial-assistance.page.

**Ta yaya zan sami takardar shaidar mutuwa wanda ke nuna dalilin mutuwar wanda ya mutu a NYC?**

Ma'aikatar Lafiya ta NYC da Kiwon Lafiyar Kwakwalwa (Ma'aikatar Lafiya ta NYC) suna ba da takardun shaidar mutuwa don mace-mace da ke faruwa a NYC (Bronx, Brooklyn, Manhattan, Queens, da Staten Island). Ana samun takardun mutuwa da zarar asibitin likita sun ba da rahoton mutuwar mutum kuma an yi rajistar lamarin ta Sashin Kiwon Lafiya na NYC.

Idan an hada da gidan jana'iza, hanya mafi sauki don samun takardar shaidar mutuwa ita ce a yi odarta daga darektan jana'izar wanda ya yi shirye-shiryen jana'izar. Daraktan jana'izar na iya yin odar takardun shaidar mutuwa a gareka har zuwa shekaru biyu bayan mutuwar mutumin.

Idan ba'a hada da gidan jana'iza ba tukuna ko kuma ba za ku iya yin odar takardar shaidar mutuwa daga darektan jana'izar ba, za ku iya yin odar ta kan layi a vitalchek.com. Duba Sashin Lafiya na NYC na Shafukan yanar gizo na Takardun Mutuwa don ƙarin bayani kan ba da odar takardar shaidar mutuwa.

**Wanene ya cancanci neman takardar shaidar mutuwa wanda ke nuna dalilin mutuwar?**

Wadanna madanganta na biye ne kawai ke iya buƙatar takaddar mutuwar da dalilin mutuwar: Ma'aurata; Abokin cikin gida; Iyaye; Yaro; 'Yan'uwan; Kaka; Jikan; Mai ba da rahoto wanda aka jera a takardar shaidar; Mutumin da ke da alhakin sarrafawa

**Nawa ne kudin takardar shaidar mutuwa?**

Kowane kwafin da aka tabbatar yana a farashin $15. Ana iya samun ƙarin kuɗi lokacin yin odar takardar shaidar mutuwa akan layi.

**Shin zan sami tabbataccen na rubutaccen tarihin mutuwar?**

Ee. Ma'aikatar Lafiya ta NYC za ta ba da tabbataccen takardar shaidar mutuwar ta asali. Takardar shaidar mutuwa ta NYC ta haɗa da fasalolin tsaro da yawa don tabbatar da cewa takardar shaidar ingantacciya ce. Idan kana da haƙƙi ga dalilin mutuwar (duba sama), kuma zaka karɓi **"**Rahoton Likita na Sirri**"** wanda ke nuna dalilin mutuwar. Wannan takardar kuma yana nuna sunan wanda ya mutu, lambar takardar shaidar mutuwa kuma an buga shi akan takardar bond.

**Ta yaya zan nemi sanadin mutuwa idan ba a rubuta dalilin mutuwar a takardar shaidar mutuwar ba?**
Don Allah nemi sanadin mutuwar lokacin da kake odar takardar shaidar mutuwar.

**Shin akwai wani kudi na daban don dalilin mutuwar?**
A'a. Babu ƙarin kuɗi don dalilin mutuwar.

**Me zan yi idan dalilin mutuwa ya nuna "a jinkirta"?**
Idan dalilin mutuwar ya nuna "an jinkirta", zaka iya musanya takardar shaidar mutuwar a cikin watanni uku na kwanan watan fitowar takardar shaidar mutuwa. An rubuta ranar bayarwa a ƙasan takardar shaidar mutuwa. Hakanan zaka iya yin odar sabon takardar mutuwar da ke nuna dalilin mutuwar a kan layi, wanda zaka karɓa da wuri fiye da musayar takardar shaidar mutuwar.

**Me yasa takardar shaidar tana nuna cewa sanadin mutuwar na dabi'a ne yayin da mutumin ya mutu daga COVID-19?**
A watan Afrilu na 2020, Cibiyoyin Kula da Cututtuka da Kariya (the Centers for Disease Control and Prevention) sun ƙaddara cewa a cikin yanayin mutuwa saboda kamuwa da COVID-19, yanayin mutuwa kusan koyaushe na dabi'a ne.

**Me zan yi idan dalilin mutuwar bai nuna COVID-19 ba?**
Ya kamata ka fara tuntuɓar ƙwararren likita ko cibiyar kula da lafiya waɗanda suka tabbatar da mutuwar don bayani game da sauya dalilin mutuwar da ke akwai don nuna COVID-19 a matsayin babban dalilin ko kuma dalilin mutuwar. Idan kai ne mai Karbar bayani da aka jera akan takaddar mutuwar ko kuma mutumin da ke da iko kan iya yin komai zaka iya mika bukata zuwa ga Ma'aikatar Kiwon Lafiya ta NYC don gyara dalilin mutuwar. Ziyarci Sashin Kiwon Lafiya na NYC Shafin yanar gizo na Gyaran Takardar Shaidar don umarni kan abinda zaka buƙaci miƙawa, a sashen Tambayoyi da Amsoshi (FAQ), "What is the process to correct a death certificate?" (Menene hanyoyin aiwatar da gyarar takardar shaidar mutuwa).

Ma'aikatar Lafiya ta NYC na iya canza sharrudan yayin da yanayin ke canzawa. **4.11.21**